komai,  kuma Mai tasarrufi a dukkan wani abu, ba Shi da abokin tarayya a cikin haka.

2- Tauhidin Uluhiyya: Shi ne imani cewa haƙiƙa Allah- tsarki ya tabbatar maSa- Shi ne abin bautawa da gaskiya, ba Shi da abokin tarayya a cikin haka, shi ne ma'anar La'ilaha illallah. Haƙiƙa ma'anarta ba bu abin bautawa da gaskiya sai Allah, dukkanin Ibadu na sallah da azumi, da wanin haka, yana wajaba a tsarkake su ga Allah Shi kaɗai, kuma ba ya halatta a juyar da wani abu daga garesu  ga waninSa.

3- Tauhidin sunaye da siffofi: Shi ne imani da dukkan abinda ya zo a a cikin Alƙur'ani mai girma, ko a cikin Hadisai ingantattu, na sunayen Allah da siffofinSa, da tabbatar da su ga Allah, Shi kaɗai, a bisa fuska mai dacewa da Shi, ba tare da canzawa, ko korewa, ko misaltawa, ko kamantawa da (halittarSa) ba; don yin aiki da faɗarSa - tsarki ya tabbatar maSa -:

﴿قُلۡ هُوَ ٱللَّهُ أَحَدٌ ١ ٱللَّهُ ٱلصَّمَدُ ٢ لَمۡ يَلِدۡ وَلَمۡ يُولَدۡ ٣ وَلَمۡ يَكُن لَّهُۥ كُفُوًا أَحَدُۢ ٤﴾

{Ka ce: "Shi ne Allah Makaɗaĩci. (1)
"Allah wanda ake nufin Sa da buƙata". (2)
"Bai haifa ba, kuma ba a haife Shi ba." (3)
"Kuma babu ɗaya da ya kasance kini a gare Shi. (4)} [al-Ikhlas: 1-4]. Da kuma faɗinSa - Mai girma da ɗaukaka -:

